# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na uku: Asarar rayuka

Wanda ya rubuta: Nkoji C. Muhoho
Wanda ya tace: Maja Braun
Wanda ya fassara: Kabir Isa Jikamshi

**'Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Bilkisu: | 'yar shekara 40 |
| Mariya: | 'yar shekara 43 |
| Hadiza: | 'yar shekara 15 |
| Sama'ila: | ɗan shekara 17 |
| Adamu: | ɗan shekara 36 |
| Dokta Husaina: | 'yar shekara 34 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, lale marhabin da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka  Karu", inda muke kawo muku ƙarin haske game da batutuwan tsabta da na cutar gudawa. A wasan da ya gabata mun tsaya inda Uncle Adamu, ma'aikacin kyautata jin daɗin jama'a kuma surukin Bilkisu, mahaifiyar jinjira Fati, ya garzaya da Fati asibiti bayan da ta kamu da cutar gudawa. Shi kuma Sama'ila, wato wan Fati, yana ci gaba da kwanciya a gado, jiki babu ƙarfi saboda cutar gudawan da yake fama da ita.

**Fitowa ta 1: A asibiti**

Bilkisu, Adamu, Hadiza

| | |
|---|---|
| **BILKISU** | Na kusa kashe 'yata. Ba zan ƙara rasa wani daga cikin iyalina ba. Da farko, baban Sama'ila ya kau, yanzu kuma 'yata. Kai! Adamu, mene ne ya kamata in yi yanzu? Me suke yi wa 'yata? |
| **ADAMU** | Bilkisu, don Allah ki kwantar da hankalinki, suna yin wasu 'yan gwaje-gwaje ne. |
| **BILKISU** | Waɗanne gwaje-gwaje? Don me ba za su ba 'yata wasu magunguna ba kawai, in ɗauke ta zuwa gida? |
| **ADAMU** | Ai, sai sun gano ko wace ƙwayar cuta ce take addabarta, sannan su iya ba ta maganin da ya cancanta. |
| **BILKISU** | Kana nufin, gamin gambizar da Mariya ta yi wa toka da ayaba, ba zai yi mata magani ba? |
| **ADAMU** | Kamata ya yi a ce Fati tana nan asibiti tun kwana bakwai bayan da ta fara nuna alamun kamuwa da cutar gudawa. Gudawa cuta ce babba, bai kamata a dogara ga maganin gida ba. |

**BILKISU** Amma kuma ƙawata Mariya ta yi amana sosai da maganin gida, inda ta riƙa gwada magunguna iri–iri. Kai! Wayyo 'yata! Hadiza, na san cewa mahaifiyarki tana da kyakkyawar niyya.

**HADIZA** Mama Bilkisu, ki daina kuka! Allah ya ba Fati lafiya!

**ADAMU** Dole sai likitoci sun gano irin lahanin da ƙwayoyin cutar suka yi wa jikinta.

**BILKISU** Kai, Allah sarki 'yata! Kawai dai ba ki yi dace da uwa ba.

**ADAMU** Shhhh! Kada ki furta haka! Ke uwa ce ta gari, ba ki dai da wani isasshen ilimi ne game da cutar gudawa da kuma yadda za ki kare 'ya'yanki.

**BILKISU** Amma… amma daga ina waɗannan ƙwayoyin cutar suka fito? Ba na ajiye ko ɗaya a gidana.

**ADAMU** Suna ko'ina.

**HADIZA** Mama Bilkisu, ki daina kuka! Suna kan hannuwanmu. Malamanmu sun ce idan mutum bai wanke hannunsa, zai iya kamuwa da cutar gudawa. Mama Bilkisu, ba na sha faɗa miki cewa mu riƙa wanke hannuwanmu ba, amma ke kuma sai ki ƙi….

**ADAMU** Hadiza, kada ki kawo wannan magana yanzu. Ina jin dai sun shirya ganinmu. Bari mu je mu ga likitocin. Mun kuwa yi sa'a, matata tana aiki yau.

**BILKISU** Wayyo Allah!

## Fitowa ta 2: A ofishin Dokta Hussaina

Bilkisu, Dr Husaina, Adamu, Hadiza

**BILKISU** Dokta Husaina! Dokta Husaina, don Allah ki faɗa mini ko 'yata za ta warware, don Allah! Za ta samu lafiya, ko kuma a'a?

**DR HUSAINA** Ko da yake jinjira Fati tana samun kulawa a asibiti, amma dole in faɗa cewa halin da take ciki yana da ban tsoro. Cutar ta yi tsanani. Me ya sa ba ku kawo ta asibiti da wuri ba?

**HADIZA** Anti Husaina, sun ƙi su saurare ni. Na shaida musu cewa, malamata ta ce…..

**ADAMU** Haba Hadiza, na ce ki bar wannan maganar fa. Bari mu ji abin da Dokta Husaina za ta ce.

**DR HUSAINA** To. Fati ta rasa ruwa mai yawa a jikinta. Mun kai ta sashen kula da marasa lafiyar da ciwonsu ya yi tsanani sosai.

**BILKISU** Wayyo Allah! Ina son ganin 'yata. Ina son ganinta ne yanzu-yanzu!

**Fitowa ta 3: A ɗakin kula da yara majiyata**

Adamu, Bilkisu

**ADAMU** Yi haƙuri mana! Ai, ga ta can a kan wancan gadon na ƙarshe.

**BILKISU** Kai! Wayyo Allah! Mene ne suka yi mata? Mene ne na yi haka? An sanya mata bututu kamar dai… kai! Mene ne suka yi mata ne?

**ADAMU** Shhhh, kar ki ruɗe. Suna yi mata magani tare da yi mata ƙarin ruwa ne ta kafar jijiyoyinta.

**BILKISU** Adamu, ina son jinjirata. Ina son ta warke. Ina son in ɗauke ta. Don Allah, don Allah! Bari mu mayar da ita gida kawai. Na yi alƙawarin zan kula da ita sosai. Na yi alƙawari.

**ADAMU** Nan ne wurin da ya fi dacewa ga wannan yarinyar a halin yanzu, nan asibiti.

**BILKISU** Wayyo!

**MAI BA DA LABARI:**

A halin yanzu dai Bilkisu ta zauna a gefen gadon jinjira Fati, tana ƙoƙarin kyautata fatan yarinyar za ta warware. A can kuma a ɗakin maziyartar asibitin, Hadiza tana yin amfani da damar zuwan nata domin yin tambayoyi game da abubuwan da ta gani a wannan sashe na jinyar yara.

**Fitowa ta 4: A ɗakin maziyarta a asibiti**

Hadiza, Dokta Husaina

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Anti Husaina, Uncle Adamu da Mama Bilkisu sun tafi ganin Fati ne? |
| **DR HUSAINA** | E, sun tafi. Amma tana jin jiki sosai. Za ki iya ganinta nan gaba, amma ba yanzu-yanzu ba. |
| **HADIZA** | Anti Husaina? |
| **DR HUSAINA** | Na'am, Hadiza? |
| **HADIZA** | Na ji suna cewa an sanya mata *drip*. Mene ne *drip*? |
| **DR HUSAINA** | Wasu lokutan idan muna rashin lafiya mai zafi, misali idan mun kamu da cutar gudawa, mukan zubar da yawancin ruwan da ke cikin jikinmu. Kuma yawancin jikinmu an yi shi ne da ruwa, ko kuma duk ruwa ne. A dangane da haka idan muka zubar da yawancinsa, jikinmu ba zai iya yin aiki ba yadda ya kamata. Kamar dai a ce ma ki mota ce babu man fetur. Don haka, dole mu taimaka wa jiki ya mayar da ruwan da ya rasa. Wannan ne ya sa likitoci suke maƙala wani bututu a jikin majiyaci domin ya riƙa kai ruwa cikin jikin. |
| **HADIZA** | Amma, don me ba za ku ba ta da kofunan ruwa ba kawai? |
| **DR HUSAINA** | Ba wai ruwa ba ne kawai ake bai wa jinjira Fati ta cikin wannan bututun. Ruwan yana haɗe da wasu magunguna da |

kayan abinci. Kin kuwa lura cewa, ko bayan gudawar da Fatu ta riƙa yi, ta kuma kasa cin abinci sosai?

**HADIZA** Oh! Yanzu-yanzun nan ta yi kuka, ta yi bayan-gida, ta yi barci, sannan ta ƙara farkawa, ta sake yin kukan da kuma wani bayan-gidan.

**DR HUSAINA** Kin gani ko, tana kuma buƙatar abinci ke nan. Tana buƙatar ƙarfin jiki da abincin da zai gina jikin, da kuma maganin da zai kashe ƙwayoyin cutar dake cikin jikinta. Tun da yake abinci bai zama cikin jikinta sosai, dole mu samo wasu hanyoyin da abincin zai zauna lokaci mai tsawo, domin jiki ya iya tatsar sinadarin da zai gina shi.

**HADIZA** Anti Husaina, kina da basira sosai. Ni ma ina son zama likita kamarki. Ina son…

**BILKISU** Husaina, Husaina! Zo da sauri, zo da sauri! Husaina! 'Yata… 'yata za ta mutu! Zo don Allah!

**HADIZA** Mene ne? Me ya faru?

**ADAMU** Husaina, yi gaggawa ki zo mana! Jikin Fati ne ya yi tsanani. Ki zo da sauri mana!

**INTERCOM** Dokta Husaina Bello, Dokta Husaina Bello! Don Allah ki hanzarta zuwa ɗakin yara. Ana neman Dokta Husaina Bello a ɗakin yara majiyata.

**MAI BA DA LABARI:**
Jinjira Fati ta shiga jerin sunayen yara masu yawa da suka halaka a sanadiyyar cutar gudawa, ɗaya daga cikin cututtukan da suke yin kisa sosai a Afirka duk da yake gudawa wata cuta ce wadda za a iya ɗaukan matakan rigakafin kamuwa da ita.

**Fitowa ta 5: A ofishin Dokta Husaina**

Hadiza, Bilkisu, Adamu, Dokta Husaina

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Fati ta rasu…. Abin kamar a mafarki. |
| **BILKISU** | Ni ce, wallahi, ni ce! Laifina ne. Kamata ya yi in ɗauki mataki tun da wuri. Yanzu ga shi na yi sanadin sake rasa rai a cikin iyalinmu. |
| **ADAMU** | Kin ga, je ki can wurin yanzu. ’Yar’uwata, ki yi haƙuri! Allah ya karɓi abin da ya bayar. |
| **HADIZA** | Lamarin babu daɗi. Ya ba da, kuma ya karɓa, bayan da aka yi fama da cutar gudawa. Da ma dai cutar gudawan aka kawar, aka bar mana Fati. |
| **DR HUSAINA** | Kamata ya yi a ce na kawo miki ziyara a kai-a kai. Da hakan ya sa na yi… |
| **ADAMU** | Husaina, don Allah kada ki ɗaura wa kanki laifi. Ni ne ya kamata a ce ina kai masu ziyara a kai-a kai. Bilkisu matar ɗan’uwana ce wanda ya rasu. Ya kamata in riƙa kula da su. Kamata ya yi na zama kusa da su sosai. |
| **HADIZA** | O, a’a! Zan mutu, Anti Husaina, zan mutu, zan mutu! Don Allah, ki taimaka! |
| **ADAMU** | Ke! Daina haka, dakata! Dakata, Hadiza! |
| **DR HUSAINA** | Ke Hadiza, don me kike jin cewa za ki mutu? |
| **HADIZA** | Na taɓa jinjira Fati. Ban wanke hannuna ba. |
| **DR HUSAINA** | Yanzu ki tafi can wurin famfo ki wanke hannuwanki. Sannan ki daina kuka, ba za ki mutu ba. Ina nan. Ni antinki ce, kuma likita. Kin gane? |
| **BILKISU** | ’Yata ta rasu, ’yata ta tafi, … |
| **HADIZA** | Sama’ila!!!! |
| **ADAMU** | Yanzu kuma mene ne? Me yake faruwa da Sama’ila? |

| | |
|---|---|
| **HADIZA** | Sama'ila, Sama'ila! Zai mutu, zai mutu! Haba, a'a Sama'ila! A'a, ba dai Sama'ila ba! |
| **DR HUSAINA** | Hadiza, me kike nufi? Mene ne? Ina Sama'ila? |
| **BILKISU** | A'a! Ba kuma za ta faɗa a kan Sama'ilana ba. Yanzu kowa ya mutu. Ni ma sai in yi addu'a Allah ya ɗauki raina, in kamu da cutar gudawa, domin ta zama sanadiyyar rasuwar 'ya'yana Baban Sama'ila, ina zuwa yanzu. |
| **ADAMU** | Haba Hadiza, ki daina kururuwa, yi mana bayani! Me yake faruwa ga Sama'ila, yana ina? Me yake damunsa? |
| **HADIZA** | Sama'ila zai mutu a kan gado a cikin gida. Shi ma cutar gudawa za ta kashe shi. |
| **DR HUSAINA** | Haba, a'a'a'a! Adamu, ɗauko mota, mu tafi! |
| **BILKISU** | … wayyo… wayyo, shaiɗan ya sake kawo ziyara gidana. Cutar gudawa,.. ke shaiɗan ce…shaiɗan ka tafi, ka san inda dare ya yi maka. |
| **DR HUSAINA** | Zo Bilkisu! Zo mu je mu ɗauko Sama'ila. |
| **BILKISU** | Ba zan iya barin jinjirata Fati ba, amma kuma ina buƙatar Sama'ila. Ba zan iya tafiya ba. Wayyo, yaya zan yi ke nan? |
| **DR HUSAINA** | Fati tana nan, ma'aikatan asibiti za su kula da gawarta. Dole mu tafi mu kuɓutar da ran Sama'ila. Bari mu tafi. Mu tafi don Allah, Bilkisu. Mu tafi mu ɗauko Sama'ila tun kafin lokaci ya ƙara ƙurewa sosai. |

**MAI GABATARWA:**

Bilkisu, abin tausayi. Yanzu kam al'amura sun yi muni sosai. Duk da haka dole ta fi nuna damuwa game da kuɓutar da wani ran, ta ƙyale ma'aikatan asibitin su kula da gawar 'yarta da ta rasu. Ya zama wajibi a tsira da rayuwar Sama'ila. Ta rasa Fati amma dole ta ɗauki matakan ganin cewa ba ta yi rashin wannan saurayin ba. Dole a hanzarta kawo Sama'ila asibiti domin ya samu

magani. Ana iya ziyartar adreshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de, domin sake sauraron wannan shiri.